# YEKUWAR

**“Kungiyar Manazarta Al’amuran Duniya kan Dorewar Zaman Lafiyar Bil-Adama”.**

Jama’a a dauka cin duniyar nan sun tsani ko basa goyon bayan tashin hankali da yaki. Suna goyon bayan abota, aminci, hakuri da juna da kuma zama lafiya. (A wata matsaya ta 52/63, shekara ta 2001 zuwa 2010 shekaru goma ne da aka cimma matsaya da cewa “Shekaru ne na neman zaman lafiya da’a rashin son tayar da husuma ga daukacin yara na duniya” na majalisar Dinkin duniya).

## Daga: Prof. Dr. Timi Ecimovic

A taron manazarta na ranar 15 ga watan Agusta 2011 aka yi a jami’ar Anstead, Sir. Prof. Dr. Major Roger Haw Boon Hong, Penang, Malaysia, SEM na cibiyar kula da Sauyin yanayi, Prof. Dr. Timi Ecimovic, zg Medosi, Kaorte, Slovenia, Prof. Dr. Dana Marie Barry (USA) da Kungiyar kula da ‘yancin yara, Hon. Ricaardoe Di Done, Montreal, Canada, Ambassador Dato’ Dr. Ang Ban Siong (Malaysia), Dr. Nixon Yap (Malaysia), Professor Tang Shui Yuan, Ciyaman na taron “Farko na Kasa-da-kasa kan kare duniya da Teku” da aka yi a Xiamen, China, da Dr. Garfield Brown, na Afrika ta kudu suka bayar da shawarar Kafa majalisar kamar haka:

A cikin wannan kungiya ta manazarta al’amuran duniya akwai majalisar gudanarwa mai suna: :Kungiyar Manazarta Al’amuran Duniya kan Dorewar Zaman lafiyar Bil-Adama”.

A takaice yana da alama kamar haka” WTP-SEM” da kuma taswira ko alama da ke kasa.



**Kungiyar Manazarta Al'amuran Duniya kan Dorewar Zaman lafiyar Bil-Adama.**

**Adireshinta shi ne korte 124, SI 6310 Izda – Isola a kasar, Slovenia.**

Jerin kungiyoyi na jama'a da ke sassa daban-daban na rayuwa kamar malamai, masana kimiyya, 'yan siyasa, ma'aikata, jami'an gudanarwa da gaggan jami'an gwamnati da sauran jama'a ke goyon bayan wannan yekuwa. Daga cikinsu akwai SEM Cibiyar Nazarin Sauyin Yanayi, alummar Jami'ar Ansted da sauran 'yan kungiyar manazarta al'ummar Duniya kan dorewar zaman lafiyar Bil-Adama da Sauransu.

Za a iya samun rubuce-rubuce kan wannan yekuwa a ayyuka daban-daban na "Dorewar ci-gaba" da "Dorewar ci-gaban Bil-Adama". A Littafi mai suna "Dorewar Ci-gaban dan Adam" Ecimovic, da Sauran masana kimiyya masu yawa a forkon karni na 21. Za a iya gani kuma ta yanar gizo mai lamba www.instut-chimatechange.si.

Magoya bayan wannan yekuwa basa biyan ko sisi. Ana sa ran da cewa majalisar Dinkin duniya, gwamnatocin kasashe, kamfanonin kasa da-kasa, makarantun kasa-da-kasa, makarantun kasashe da sauransu za su goyi bayan aiki kan ci-gaban bil-Adama.

Yekuwar tana samar da'yanci da neman mutunta bil-Adama daga gwamnatoci da kungiyoyin al'umma na duniya miliyan (7000000000 ko sama da haka). Buri anan shi ne kai wa wani mataki a duniya na ci-gaban al'umma. Wannan ci-gaba ne na bil-Adama da zai tashi daga ci-gaban al'umma zuwa ci-gaban al'umma mai dorewa bisa ga wasu dabaru. Majalisar dinkin duniya gami da rassanta Musamman UNEP da UNESCO ana yi masu Maraba zuwa shiga wannan yekuwa ta dorewar ci-gaban bil-Adama.

Rayuwarmu ko ta dan Adam gajeriya ce, wacce ke bakutar a yi ta cikin farin ciki, walwala da ma'ana, saboda haka mu ginshiki ne na kafuwar" rayuwar dan Adam" Wajibi ne mu goyi bayan rayuwa da ci-gaban dan Adam. Saboda burinmu ne hada kan bil-Adama a duk in da suke a duniya wanda ya hada da kakanninmu da suka shude da kuma yaran da za mu Haifa nan gaba. A matsayinmu na 'yan Adam tilas ne mu kula da junanmu da kuma wadanda za mu haifa nan gaba.

"Wannan Kungiya Ta manazarta" al'amuran duniya kan dorewar zama lafiyar bil-Adama" tana samar da wani bigire na jama'a masu (Sha'awar fannoni kamar na zane-zane, kimiyya da abubuwan da suka shafi al'adu da yekuwar neman zaman lafiya) su hadu su yi aiki tare.

Makasudin aiki a wannan bigire shi ne samar da wata dama ta fahimtar juna da hakuri da juna tsakanin jama'a daban-daban na duniya da kuma bayar da gudummawa ta hanyar samar da da'a zaman lafiya a duniya. Muna yi wa jama'a da kungiyoyin jama'a na duniya a duk in da suke maraba, ba tare da nuna bambancin kabila, jinsi, harshe ko addini ba. Aikin "Kungiyar manazarta na duniya" kan dorewar zaman lafiyar bil-Adama" ta jingina ne bisa ga mutunta

‘yancin yana da alaka da kungiyar kulawa da ‘yancin yara na majalisar dinkin duniya UNESCO “Akidar zama Lafiya”.

“Alhakin da ya rataya kan manazarta na duniya kan dorewar zaman lafiyar bil-Adama” shi ne samar da wata dama ga dukkan kungiyoyin da ba na gwamnati ba, ma’aikatun gwamnati, kungiyoyi na kimiyya da na al’adun gargajiya, da cibiyoyin nazari, kungiyoyi mabanbanta, ofisoshin adana kayan tarihi, jami’o’i, gidauniyoyi, kungiyoyi, kungiyoyi na ’yan kasuwa da Sauran ma’aikatu.  Haka kuma kungiya ce ta mutane daban-daban wadanda suka sami kansu tsundum a harkokin habaka abubuwan da suka shafi al’adun gargajiya, tatsuniyoyi da kuma abubuwan da suka shafi kimiyya.

Baya ga wadannan ayyuka na wannan kungiya tamu da suka shafi kimiyya da fasaha, har ila-yau muna cudanya da kungiyoyi na siyasa da na al’adun gargajiya. Da yawa daga cikinmu sun koya har sun girma daga zama sababbin mambobi na **“kungiya manazarta al’amuran duniya kan dorewar zaman lafiyar Bil-Adama”.**

Yekuwar ta samar da ‘yanci, kuma tana neman ‘yanci ga kowanin bil-Adama a doron kasa: kimanin biliyan bakwai.  Burinmu shi ne cimma wani mizani na ci-gaban al’umma a duniya.  Wannan irin  ci-gaba wata hijara ce daga ci-gaban kadai zuwa ci-gaban al’umma mai dorewa.

Ana yi wa rassan majalisar dinkin duniya kamar reshenta da ke kula da ilimi (UNEP) ada mai kula harkokin yara maraba cikin wannan yekuwa na dorewar ci-gaban bil-Adama.  Za a kuma kai yekuwar ga sassa daban-daban na duniya.

Muna sa ran duk ’yan wannan kugiya na manazarta ci-gaban al’umma na da hakkin taimakawa idan an nemi haka.  Da yawa daga cikin cibiyon al’adu, da na shakatawa, da kuma na makarantun kimiyya (na kasa da kuma na kasa da kasa) za su bayar da gudunmawarsu domin tallafawa wannan cibiya da ke da akida irin tasu.

Mun yi imani da cewa “Kungiyar manazarta, masu rajin dorewar zaman lafiyar bil-Adama” ba kawai sun tsaya ba ne kan fafutukar ‘yancin dan Adam, burinmu ya hada da cudanya ta hanyar shirya bukin al’adun gargajiya wanda a zahiri ke bayar da wata dama ta warware matsalolin rayuwa a wannan zamani.

Wadanda suka kafa “Kungiyar manazarta al’amuran duniya kan dorewar zaman lafiyar bil-Adama” ta karkasa ayyukanta domin tallata kanta a idon duniya.  Ga kason kamar haka:

**Rabe-rabe**

1. Sigar al’adun gargajiya
2. Muhimmancin al’adun gargajiya a wannan zamani.
3. Al’adun gargiya da bambance-bambancensu
4. Al’adun gargajiya da ‘yancin al’ada
5. Al’adun gargajiya da nau’o ‘insa
6. Shiri domin ciyar da ko bunkasa al’adun gargajiya ta hanyar nazarin al’adu da yin mu’amala da sauran al’adu, da hadin kai, da gudanar da taro na al’adu mabambanta da kuma bunkasa cibiyoyin al’adun gargajiya.

1. **Sigogin Al’adun Gargajiya.**

Al'adun gargajiya hoto ne na rayuwar al'umma da aka san jama'a na yi shekaru aru-aru tsakanin mutane da ke da al'adu daban-daban ta yadda ba za a ware wani ba, saboda irin nasa al'adar da ta saba da ta wasu, ko saboda alakar da al'adar ke da ita da addini.

2. **Muhinnancin al'adun gargajiya awannan zamanin**

Tun Samun ci-gaban zamani da aka yi ta fannin rayuwa da masana'antu, wannan zamanin ya fuskanci matsaloli da dama a fannin al'adu, bala'o'i, matsananciyar gasa a fannin kasuwanci, rashin adalci wajen raba dukiya, yawaita kawar da jinsi, baiwa abin duniya muhimmanci marmakon karantarwar addini wannan ya jawo tsanani sosai a rayuwar 'yan adam. Duk wadannan matsalolin za'a iya amfani da al'ada wajen warware su a cikin zamanin nan namu. Musamman a al'adun mutanen Confucian da ke a yankin Asiya ya ba da Muhimmanci sosai a fannin tsoron 'Ubangiji' da yin 'da'a sune ginshikai, wadannan Muhimman abubuwa ginshikai ne a wajen kawar da zaman dar-dar da kiyayya a tsakanin al'umma, kuma za su taimaka wajen dawowa da martabar bil'adama.

3. **Bambance-Bambancen al'adu**

Al'ada ta samu ne sakamakon sadarwa da mu'amala a tsakanin jinsin bil'adama don tarayya da suka yi a muhalli daya, shi ne ke wakiltan mutane kasashe da bangarori. Don haka za'a iya cewa al'adu Mabambanta ne a duniya (kowa da nasa).

4. **'Yancin bin al'adu**

'Yan kasa na da 'yancin siyasa da sha'anin bunkasa harkokin jin dadin rayuwarsu da kuma 'yancin al'adu. Dole ne a ba 'yan kasa damar cin moriyar al'adunsu na gargajiya da kuma ci-gaba da zamani ya zo da shi. A yanzu ana daukan al'adu wani abin kanyauci shi ya sa wasu ba su mutunta

shi, don inganta al’adun mutane a samar da dokoki da za su taimaka wa mutane bin al’adunsu ko’ina kuma a kowane lokaci.

5. **Al’adunka da na wasu**

Mu’amalar da muke yi da al’adun wasu za ta sa mu fahimci wasu al’adun da ba namu ba, yin hakan kan kara taimaka mana fahimtar wasu bangarorin da al’adunsu. Ana son a kara ba da muhimmanci kan al’ada da fasaha ana bukatar hakan ne domin zai taimaka wajen adana surar mutanen yankin.

6. **K’udurin bunkasa al’adun gargaji**

Al’ada na da Muhimmanci Sosai Kamar yadda Muka nuna a nan sama, don adana shi da bunkasarsa, an ba da shawarwari nan kasa kamar haka. An ba da shawarar cewa gwamnatoci, kungiyoyi masu zaman kansu da al’ummu su yi hadin kai don cimma wannan burin.

(I) **Musayan al’adu da hadin kan bangarori**

Musayan al’adu na da daraja wajen sanin al’adun wasu. Har-wa-yau wannan musayan akan yi shi ne ba tare da hikima ba kuma cikin gaugawa, ba tare da barin mutane su musanya al’adar ba kan hankali. Don al’ummu su morewa ‘yancin bin al’adarsu har su yi Masaya da wasu, to ana so a samar da hanya mai sauki da za ta taimaka wajen yin hakan. Gwamnatoci, kungiyoyi masu zaman kansu da al’ummu su ba wannan Muhimmanci.

(II) **Tarurruka akai-akai masu alaka da al’adu.**

Arika yin taron akai-akai don bunkasa fahimtar al’ada ta fannin da za ta taimaki bil’adama cimma zaman lumana ko’ina a cikin duniya, don ajiyar al’adu daban-daban da zai taimaki kasa da al’umma ba da Muhimmanci ga al’adunsu.

(III) **Bunkasa fannin abin da ya shafi al’ada**

Don riko ga al'ada a yi amfani da ita kuma a rayu rayuwa ta zamani, amfaninsa a tabbatar ya samu ga kowa, kuma a karfafa rayuwa ta cikin al'umma. Ana bukatar raya al'adu irin na tatsuniya da fasaha su tafi tare da al'adu. Sha'anin al'adu ya shafi rayuwa ta zamani don haka mu san kowanne mai cin gashin kansa ne don haka ana son ya warkar da kishi ta fannin al'adu da al'umma ke fama da ita.

Wannan bayanan ginshikai ne ba wai kawai kwarewa ba ne a fannin sanin aiki

Hakan na wakiltan al'ummar bil'adama ta duniya da ke cikin Karin fuskantar hadari, don haka ana bukatar gobe mai inganci ta hanyar kula da muhalli da ilimi. Wannan ikirarin shi ne farkon hanya shararra ta cimma ci-gaban bil'adama mai dorewa, da kuma hadin kan bil'adama da ke zaune a bayan kasa. Wannan shi ne gudunmawar da za mu bayar ga rayuwar zuri'armu. Majalisar dunkin duniya ta gwamnatocin kasashe dole ne su daina nuna halin ko-in-kula, su samar da hadin kai da ake bukata da zai kawo canje-canje da zai bunkasa ci-gaban bil'adama mai dorewa. Muna bukatar wani ja-makafi na duniya, ingantaccen shugabanci na duniya, da wasu abubuman da duniya ke mutuntawa.

Lokacin nan namu ana bukatar ayyuka tukuru domin dorewar ci-gaban rayuwa. Har-lla-yau muna bukatar jagorancin al'ummar duniya, karkashin ba da gudunmawar daidaikunmu da jama'a baki daya. Dole ne mu goyi bayan ingantatattun ilimin kimiyya da ya shafi kimiyyar bil'adama, haka nan ana bukatar karfafa biyayya, zaman lafiya, yin aikin kwarai, da hikima.

Ina fatar ganin duniya na karfafa aiki da ra'a-yin wannan ikirarin don dorewar ci-gaban bil'adama.

**Farfesa. Dr. Timi Ecimovic.**